IslamHouse.com

# SHIKA-SHIKAI GUDA UKU



Muhammad Bin Abdul Wahhab

KASAR MASARAWTAN LARABAWA TA SAUDIA
MINISTAN ILIMI NA KOLI
JAMIAR ISLAMIA TA MADINA ALMUNAWWARA
BARIKIN BINCIKEN ILIMI
RESHEN TARJAMA



www.iu.edu.sa

# SHIKA-SHIKAI GUDA UKU

*Walla Fa war:*
*Limami, shehu Muhammad bin Abdul-Wahab*

*Allah Ya rahmance shi*

*Tarjamar*
*Munamadu nur Abdurhman Da Idrissa Yahaya*

المملكة العربية السعودية
وزارة التعليم العالي
الجامعة الإسلامية بالمدينة المنورة
عمادة البحث العلمي
قسم الترجمة



www.iu.edu.sa

# الأصول الثلاثة وأدلتها

تأليف / الإمام العلامة الشيخ

## محمد بن عبد الوهاب

( رحمه الله )

بلغة

الهوسا

ترجمة/ محمد نور عبد الرحمن و إدريس يحي يوسف

بسم الله الرحمن الرحيم

***Da sunan Allah, Mai Rahama, Mai Jin kai***

# SHIKA-SHIKAI GUDA UKU

***Ka sani, Allah Ya rahamce ka, cewa sanin mas'aloli guda hudu yana wajaba akan mu:***

Na farko: Ilimi, shine sanin Ubangiji, da sanin AnnabinSa, da sanin addinin Musulunci tare da dalilansa.

Na biyu: yin aiki dashi.

Na uku: yin kira zuwa gareshi.

Na hudu: hakuri akan curtarwa.

Dalili kuwa shine fadar Ubangiji Madaukakin Sarki:

﴿ بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ . وَٱلۡعَصۡرِ ۝١ إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لَفِي خُسۡرٍ ۝٢ إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلۡحَقِّ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلصَّبۡرِ ۝٣ ﴾ [سورة العصر]

{Da sunan Allah, Mai Rahama, Mai Jin kai, ina rantsuwa da zamani, lalle mutum yana cikin hasara, face wadanda suka yi imani , kuma suka aikata ayyukan kwarai, kuma suka yi wa juna wasiyya da bin gaskiya, kuma suka yiwa juna wasiyya da yin hakuri.}

Imam AsShafi'i – Allah Ya rahamce shi – ya ce: "da ace Allah bai saukar da wata hujja akan halittarSa ba face wannan sura, da ta ishe su."

﴿ فَٱعۡلَمۡ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ وَٱسۡتَغۡفِرۡ لِذَنۡبِكَ ﴾ [سورة محمد الآية ١٩]

Buhari – Allah Ya rahamce shi – ya ce: "'Babi': Ilimi yana gaban magana da aiki. Dalili shi ne fadar Allah Madaukaki: ((ka sani cewa, babu Abin bautawa face Allah, kuma kanemi gafara ga zunubinka))} - sai Ya fara da ilimi kafin, magana da aiki."

Ka sani – Allah Ya ramahamce ka – cewa sanin wadannan mas'aloli guda uku, da aiki da su ya wajaba akan kowane musulmi namiji da mace:

**Na farko**: Lalle Allah ne Ya haliccemu, Ya arzutta mu, kuma bai barmu haka ba, amma Ya aiko mana da Manzo, duk wanda ya yi ma sa biyayya zai shiga Aljannah, wanda ya saba ma sa zai shiga wuta.
Dalili kuwa shi ne, fadar Allah Madaukaki:

﴿ إِنَّآ أَرۡسَلۡنَآ إِلَيۡكُمۡ رَسُولٗا شَٰهِدًا عَلَيۡكُمۡ كَمَآ أَرۡسَلۡنَآ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ رَسُولٗا ١٥ فَعَصَىٰ فِرۡعَوۡنُ ٱلرَّسُولَ فَأَخَذۡنَٰهُ أَخۡذٗا وَبِيلٗا ١٦ ﴾ [سورة المزمل]

{Lalle Mun aika wani manzo zuwa gare ku, mai shaida a kanku, kamar yanda muka aika wani manzo zuwa ga Fir'auna. Sai Fir'auna ya sabawa manzon, saboda haka sai Mu ka kama shi, kamu mai tsanani.}

**Na biyu**: Allah bai yarda a hada wani tare dashi a cikin ibadarSa ba, ko da ya kasance mala'ika ne makusanci, ko kuma Annabi manzo.

Dalili shi ne fadar Ubangiji Madaukaki Sarki:

﴿ وَأَنَّ ٱلۡمَسَٰجِدَ لِلَّهِ فَلَا تَدۡعُواْ مَعَ ٱللَّهِ أَحَدٗا ١٨ ﴾ [سورة الجن]

((Kuma lalle wuraren sujuda na Allah ne, saboda haka ka da ku kira wani tare da Allah (a cikinsu)))

**Na uku**: Cewa duk wanda yayi biyayya ga manzon Allah, kuma ya kadaita Allah, bai halatta yaso wanda ya ke kiyayya da Allah da manzonSa ba, ko da kuwa ya kasance mafi kusancin makusanta gare shi.

Dalili kuwa shine fadar Allah Madaukakin Sarki:

﴿ لَّا تَجِدُ قَوۡمٗا يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ يُوَآدُّونَ مَنۡ حَآدَّ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَوۡ كَانُوٓاْ ءَابَآءَهُمۡ أَوۡ أَبۡنَآءَهُمۡ أَوۡ إِخۡوَٰنَهُمۡ أَوۡ عَشِيرَتَهُمۡۚ أُوْلَٰٓئِكَ كَتَبَ فِي قُلُوبِهِمُ ٱلۡإِيمَٰنَ وَأَيَّدَهُم بِرُوحٖ مِّنۡهُۖ وَيُدۡخِلُهُمۡ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ رَضِيَ ٱللَّهُ

عَنۡهُمۡ وَرَضُواْ عَنۡهُۚ أُوْلَٰٓئِكَ حِزۡبُ ٱللَّهِۚ أَلَآ إِنَّ حِزۡبَ ٱللَّهِ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ﴿٢٢﴾ [سورة المجادلة]

((Ba za ka samu mutane masu yin imani da Allah da ranar lahira su na soyayya da wanda ya saba wa Allah da manzonsa ba, ko da sun kasance ubanninsu ne ko diyansu ko yan uwansu, ko danginsu, wadannan Allah Ya rubuta imani a cikin zukatansu, kuma Ya karfafa su da wani ruhi daga gare shi, kuma zai shigar da su a gidajen Aljannah, koramu na gudana karkashin su, su na masu dawwama a cikinsu. Allah Ya Yarda da su kuma sun yarda da shi, wadannan su ne kungiyar Allah. To, lalle kungiyar Allah su ne masu rabauta.))

Ka sani (Allah Ya shiryar da kai zuwa ga da'arSa), cewa hanya madaidaiciya, hanyar Annabi Ibrahim ita ce: ka bautawa Allah shi kadai, ka na mai tsarkake addini gare Shi; wannan shi ne Allah Ya umurci dukkan mutane, kuma Ya halicce su domin sa, Allah Ya ce:

﴿ وَمَا خَلَقۡتُ ٱلۡجِنَّ وَٱلۡإِنسَ إِلَّا لِيَعۡبُدُونِ ﴿٥٦﴾ ﴾ [سورة الذاريات]

((Ban halicci Aljanu da mutane ba sai don su bauta miNi))

Abinda ake nufi da "su bauta miNi" shi ne "su kadaitaNi da ibada."

Kuma babban abinda Allah Yayi umurni da shi shine tauhidi. Kuma ma'anarsa: "kadaita Allah da ibada".

Kuma babban abinda Allah Yayi hani da shi shi ne: "Shirka", ma'anar kuma Shirka: "kiran wani (banda Allah) tare da Shi (Allah)".

Dalili shi ne fadar Allah Madaukakin Sarki:

﴿ وَٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَلَا تُشۡرِكُواْ بِهِۦ شَيۡـٔٗاۖ ٣٦﴾ [سورة النساء الآية ٣٦]

((ku bauta wa Allah, kada ku hada wani da shi))

Idan a ka ce maka: *me ne ne shika-shikai guda uku wadanda ya wajaba mutum ya sansu?*

Kace: Bawa ya san Ubangijinsa, da addininsa, da Annabinsa *Muhammad* tsira da amincin Allah su tabbata agare shi.

Idan aka ce maka: *Wane ne Ubangijinka?*

Kace*: Allah ne Ubangijina, Wanda Ya rene ni, kuma Ya reni dukkan talikai da ni'imarSa, Shi ne abin bautata, ba ni da wani abin bauta sai Shi.*

Dalili shi ne fadar Allah:

﴿ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ۝٢ ﴾ [سورة الفاتحة]

((Godiya ta tabbataga Allah Ubangijin talikai)) kuma duk wanda ba Allah ba, shi ake kira taliki, kuma ni daya ne daga cikinsu.

Idan a ka ce maka: *dame kasan Ubangijinka?*

Sai kace : *da ayoyinsa, da kuma halittunSa.*

Daga cikin ayoyinSa, akwai: dare, da wuni da Rana, da Wata, da sammai bakwai, da kassai bakwai da abinda ke cikinsu.

Dalili shi ne fadar Allah Madaukaki:

﴿ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِ ٱلَّيۡلُ وَٱلنَّهَارُ وَٱلشَّمۡسُ وَٱلۡقَمَرُۚ لَا تَسۡجُدُواْ لِلشَّمۡسِ وَلَا لِلۡقَمَرِ وَٱسۡجُدُواْ لِلَّهِ ٱلَّذِي خَلَقَهُنَّ إِن كُنتُمۡ إِيَّاهُ تَعۡبُدُونَ ۝٣٧ ﴾ [سورة فصلت]

((Kuma akwai daga ayoyinSa, dare, da yini,da rana da wata, kada ku yi sujada ga rana,kuma kada kuyi ga wata, kuyi sujada ga Allah wanda ya halitta su, idan kun kasance shine kuke bauta wa.))

Da kuma fadar Allah Madaukaki:

﴿ إِنَّ رَبَّكُمُ ٱللَّهُ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ فِى سِتَّةِ أَيَّامٍ ثُمَّ ٱسْتَوَىٰ عَلَى ٱلْعَرْشِ يُغْشِى ٱلَّيْلَ ٱلنَّهَارَ يَطْلُبُهُۥ حَثِيثًا وَٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ وَٱلنُّجُومَ مُسَخَّرَٰتٍۭ بِأَمْرِهِۦٓ ۗ أَلَا لَهُ ٱلْخَلْقُ وَٱلْأَمْرُ تَبَارَكَ ٱللَّهُ رَبُّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٥٤﴾ ﴾ [سورة الأعراف]

((Lalle ne Ubangijinku Allah ne, wanda ya halitta sammai da kasa a cikin kwanaki shida, sa annan kuma yadaidaita a kan Al'arshi, Ya na sanya dare ya rufe yini, ya na neman sa da gaggawa, kuma rana da wata da taurari horarru ne da umurninsa. To, da halitta da umurni Na sa ne, albarka ta tabbata ga Allah Ubangiji halittu!))

Ubangiji shine abin bauta.

Dalili shi ne fadarSa, Madaukaki:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱعْبُدُوا۟ رَبَّكُمُ ٱلَّذِى خَلَقَكُمْ وَٱلَّذِينَ مِن قَبْلِكُمْ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ﴿٢١﴾ ٱلَّذِى جَعَلَ لَكُمُ ٱلْأَرْضَ فِرَٰشًا وَٱلسَّمَآءَ بِنَآءً وَأَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَخْرَجَ بِهِۦ مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ رِزْقًا لَّكُمْ ۖ فَلَا تَجْعَلُوا۟ لِلَّهِ أَندَادًا وَأَنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿٢٢﴾ ﴾ [سورة البقرة]

((Ya ku mutane! Ku bauta wa Ubangijinku, wanda ya halicce ku, ku da wadanda suke daga gabaninku,

tsammaninnku, ku kare kanku! Wanda Ya sanya mu ku kasa shimfida, kuma sama gini, kuma ya saukar da ruwa daga sama, sa annan ya fitar da abinci daga dyan itace game da shi saboda ku. Saboda haka kada ku sanyawa Allah wasu kishiyoyi, alhali kuwa ku na sane.”

> Ibn kathir (Allah Ya rahamce shi) ya ce:
> “Mahaliciin wadannan abubuwa shine ya dace a yi masa Ibada.”

Duka irin dangogin ibadar da Allah yayi umurni dasu a na yin su ne domin Allah, kamar: *Islam* (Musulunci), da Imani, da *Ihsani,* haka kuma adu’a, da tsoro, da fata, da tawakkali, da fata, da fargaba, da kankantar da kai, da maida al’amari (zuwa ga Allah), da neman Taimako (daga Allah), da neman tsari, da neman agaji, da yin yanka, da daukar alkawalin yin wata ibada (bakance), dukkan wadannan ibadodin da wasunsu wadanda bamu zana ba.

Dalili akan haka shine fadar Ubangiji Madaukaki:

﴿ وَأَنَّ ٱلۡمَسَٰجِدَ لِلَّهِ فَلَا تَدۡعُواْ مَعَ ٱللَّهِ أَحَدٗا ١٨ ﴾ [سورة الجن]

kuma lalle ne wuraren na allah ne , saboda haka kada kukira kowa tare da allah [da su, a cikinsu].

﴿ وَمَن يَدۡعُ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ لَا بُرۡهَٰنَ لَهُۥ بِهِۦ فَإِنَّمَا حِسَابُهُۥ عِندَ رَبِّهِۦٓۚ إِنَّهُۥ لَا يُفۡلِحُ ٱلۡكَٰفِرُونَ ١١٧ ﴾ [سورة المؤمنون ]

((Wanda ya kira tare da Allah, wadansu abubuwan bautawa na dabam, ba yana da wani dalili game da shi (kiran) ba, to, hisabinsa yana wurin Ubangijinsa kawai, lalle ne, kafirai ba sa cin nasara)).

Kuma ya zo cikin Hadisi cewa "الدعاء مخ العبادة" Adu'a ita ce bargon ibada.

Dalili shi ne fadarSa Madaukaki:

﴿ وَقَالَ رَبُّكُمُ ٱدۡعُونِيٓ أَسۡتَجِبۡ لَكُمۡۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَسۡتَكۡبِرُونَ عَنۡ عِبَادَتِي سَيَدۡخُلُونَ جَهَنَّمَ دَاخِرِينَ ٦٠ ﴾ [سورة غافر]

((Kuma Ubangiji yace: ku kira ni in karba muku, lalle wadanda ke kangara daga barin bauta mini zasu shiga Jahannama su na kaskantattu)).

Dalili akan jin tsoron Ubangiji fadar Allah Madaukaki Sarki :

﴿ ...فَلَا تَخَافُوهُمۡ وَخَافُونِ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ١٧٥ ﴾ [آل عمران]

((To, kada ku ji tsoronsu, kuji tsoro Na, idan kun kasance masu imani)).

Dalili akan kyakkyawan fata a wurin Allah: fadarSa Madaukaki:

﴿ فَمَن كَانَ يَرۡجُواْ لِقَآءَ رَبِّهِۦ فَلۡيَعۡمَلۡ عَمَلٗا صَٰلِحٗا وَلَا يُشۡرِكۡ بِعِبَادَةِ رَبِّهِۦٓ أَحَدَۢا ١١٠ ﴾ [سورة الكهف]

((Don haka, duk wanda ya kasance yana fatan haduwa da Ubangijinsa, to, sai ya yi aiki na kwarai. Kuma kada ya yi tarayya da kowa ga bauta wa Ubangijinsa)).

Dalili akan dogara da Allah:

﴿ وَعَلَى ٱللَّهِ فَتَوَكَّلُوٓاْ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ٢٣ ﴾ [سورة المائدة ٢٣]

((Ku dogara ga Allah idan kun kasance muminai))

Kuma Allah Madaukaki Ya ce:

﴿ وَمَن يَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِ فَهُوَ حَسۡبُهُۥٓ ﴾ [سورة الطلاق ٣]

((Wanda ya dogara ga Allah, to Allah Ya isar ma su.))

Dalili a kan kwadayi, da fargaba, da kankantar da kai ga Allah shi ne, fadar Ubangiji Madaukakin Sarki:

﴿ ...إِنَّهُمۡ كَانُواْ يُسَٰرِعُونَ فِي ٱلۡخَيۡرَٰتِ وَيَدۡعُونَنَا رَغَبٗا وَرَهَبٗاۖ وَكَانُواْ لَنَا خَٰشِعِينَ ٩٠ ﴾ [سورة الأنبياء]

((Lalle ne sun kasance su na gaggawa zuwa ga ayyukan alheri, kuma suna rokonMu, cikin fata da tsoro, kuma sun kasance masu tsoron (saunar aikata sabo) gare Mu.))

Dalili a kan tsoron Allah, shi ne fadarSa, Madaukaki:

﴿ ...فَلَا تَخۡشَوۡهُمۡ وَٱخۡشَوۡنِي ﴾ [سورة البقرة ١٥٠]

“ Kada kuji tsoronsu, kuji tsoroNa”.

Dalili akan maida al’amura zuwa ga Allah:

﴿ ... وَأَنِيبُوٓاْ إِلَىٰ رَبِّكُمۡ وَأَسۡلِمُواْ لَهُۥ... ﴾ [سورة الزمر ٥٤]

((Ku mayar da al’amari zuwa ga Ubangijinku, kuma ku sallama masa.))

Dalili akan neman taimako a gurin Allah shi ne, fadar Allah Madaukaki:

﴿ إِيَّاكَ نَعۡبُدُ وَإِيَّاكَ نَسۡتَعِينُ ۝٥ ﴾ [سورة الفاتحة]

((Kai kadai mu ke bautawa, kuma gareKa kadai muke neman taimako.))

A cikin hadisi kuma: (( إذا استعنت فاستعن بالله )) Wato: "Idan za ka nemi taimako, ka nemi taimakon Allah.”

Dalili a kan neman tsari daga wurin Allah, shi ne fadarSa, Madaukaki:

﴿ قُلۡ أَعُوذُ بِرَبِّ ٱلنَّاسِ ۝١ مَلِكِ ٱلنَّاسِ ۝٢ ﴾ [سورة الناس]

((Ka ce: “Ina, neman tsari ga Ubangijin mutane, Mamallakin mutane.”))

Dalili a kan neman agaji daga Ubangiji; fadar Allah Madaukakin Sarki:

﴿ إِذۡ تَسۡتَغِيثُونَ رَبَّكُمۡ فَٱسۡتَجَابَ لَكُمۡ ﴾ [سورة الأنفال ٩]

((Ku tuna lokacin da ku ke neman taimakon Ubangijinku, sai ya karba muku.))

Dalili a kan yin yanka domin Allah, fadar Ubangiji Madaukaki:

﴿ قُلۡ إِنَّ صَلَاتِي وَنُسُكِي وَمَحۡيَايَ وَمَمَاتِي لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ۝١٦٢ لَا شَرِيكَ لَهُۥۖ وَبِذَٰلِكَ أُمِرۡتُ وَأَنَا۠ أَوَّلُ ٱلۡمُسۡلِمِينَ ﴾ [سورة الأنعام]

((Ka ce: lalle ne Sallah ta, da baikona, da rayuwata da mutuwata, na Allah ne Ubangijin talikai. Babu abokin tarayya a gare shi, kuma da wancan aka umarce ni, kuma ni ne farkon masu sallamawa.))

Ya tabbata a *Sunnah*, cewa, Annabi ﷺ ya ce:

(( لعن الله من ذبح لغير الله )) الحديث

“Allah ya la’anci masu yanka domin wanin Allah.”

Dalili akan umurni da cika alwashi, shi ne fadar Allah Madaukaki:

﴿ يُوفُونَ بِٱلنَّذۡرِ وَيَخَافُونَ يَوۡمٗا كَانَ شَرُّهُۥ مُسۡتَطِيرٗا ۝٧ ﴾

[سورة الإنسان]

Wato: “Suna cika Alwashin da suka dauka (tsakaninsu da Allah) kuma suna tsoron wani yini wanda sharrinsa yakasance mai tartsatsi ne”.

Tushe Na Biyu:
**Sanin Addinin Musulunci Tare Da Dalilansa.**

Abin nufi a nan: Dayanta Allah, tare da kadaita shi da biyayya, da barin shirka da kin ma su yin ta. Wannan kuma ya kasu kashi uku, su ne: *Musulumci*, da *Imani*, da *Ihsani* kuma kowane kashi yana da rukunai.

Kashi Na Farko: Rukunnan Musulunci biyar ne:

1. Shaidawa babu wani abin bautawa da gaskiya sai Allah, kuma hakika Annabi Muhammad manzonsa ne.
2. Tsaida *Sallah.*
***3.*** Bada *Zakkah.*
4. Yin Azumin Ramadhan.
5. Yin aikin *Hajji*.

Dalili a kan yin Shahada shi ne, fadar Allah madaukakin Sarki:

﴿ شَهِدَ ٱللَّهُ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ وَأُوْلُواْ ٱلْعِلْمِ قَآئِمَۢا بِٱلْقِسْطِۚ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ﴿١٨﴾ ﴾ [سورة آل عمران]

“Allah ya shaida cewa: lalle ne ba bu abin bauta bisa cancanta face shi; Mabuwayi, Mai Hikima.”

Abin nufi a nan: ba bu abin bautawa da bisa cancanta sai Allah shi kadai. Don haka ((لا إله إلا الله)) ta kore duk wani abin bauta banda Allah; sannan kuma ((إلا الله)) ta tabbatar da ibada a gareShi ba tare da waninSa ba, kamar yanda ba Shi da abokin tarayya a MulkinSa. Dalili a kan wannan fassarar shi ne fadar Allah Madaukaki:

﴿ وَإِذْ قَالَ إِبْرَٰهِيمُ لِأَبِيهِ وَقَوْمِهِۦٓ إِنَّنِى بَرَآءٌ مِّمَّا تَعْبُدُونَ ﴿٢٦﴾ إِلَّا ٱلَّذِى فَطَرَنِى فَإِنَّهُۥ سَيَهْدِينِ ﴿٢٧﴾ وَجَعَلَهَا كَلِمَةًۢ بَاقِيَةً فِى عَقِبِهِۦ لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ﴿٢٨﴾ ﴾ [ سورة الزخرف]

((…lokacin da Ibrahim ya ce wa abbansa da mutanensa: lalle ni mai barranta ne daga abin da ku ke bautawa .Face wanda ya kagi halitta ta, to lalle Shi ne zai shiryar da ni.))

Da kuma fadar Allah Madaukaki:

﴿ قُلۡ يَٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ تَعَالَوۡاْ إِلَىٰ كَلِمَةٖ سَوَآءِۭ بَيۡنَنَا وَبَيۡنَكُمۡ أَلَّا نَعۡبُدَ إِلَّا ٱللَّهَ وَلَا نُشۡرِكَ بِهِۦ شَيۡـٔٗا وَلَا يَتَّخِذَ بَعۡضُنَا بَعۡضًا أَرۡبَابٗا مِّن دُونِ ٱللَّهِۚ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَقُولُواْ ٱشۡهَدُواْ بِأَنَّا مُسۡلِمُونَ ٦٤ ﴾

[سورة آل عمران]

((Ka ce: ya ku mutanen littafi (Ai yahudu da nasara) ku tafo zuwa ga kalma mai daidaitawa a tsakanin mu da ku; kada mu bautawa kowa face Allah. Kuma kada mu hada kome da shi kuma kada sashenmu ya riki sashe Ubangiji, baicin Allah. To, idan sun juya baya sai ka ce: “kuyi shaida cewa lalle ne mu masu sallamawa ne.”))

Dalilin shaidawa Annabi *Muhammad* manzon Allah ne fadar Ubangiji:

﴿ لَقَدۡ جَآءَكُمۡ رَسُولٞ مِّنۡ أَنفُسِكُمۡ عَزِيزٌ عَلَيۡهِ مَا عَنِتُّمۡ حَرِيصٌ عَلَيۡكُم بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ رَءُوفٞ رَّحِيمٞ ١٢٨ ﴾ [سورة التوبة]

((Lalle ne, hakika, Manzo daga cikinku, ya je muku. abin da ku ka wahala da shi mai nauyi ne a kan sa. Mai kwadayi ne saboda ku ga muminai mai tausayi ne, mai jin kai.))

Kuma ma’anar yin shaida da cewar Muhammad ﷺ manzon Allah ne, a yi ma sa biyayya akan Abin da yayi Umarni da shi; da gaskata shi a kan abin da ya

bayar da labari, da nesantar abinda ya hana, kuma ya tsawata a kai, kuma kada a bautawa Allah sai da abinda ya shar'anta (wato ya hukumta).

Dalilin akan yin *Sallah* , da bada *Zakkah* da kuma tafsirin tauhidi shi ne, fadar Allah Madaukaki:

﴿ وَمَآ أُمِرُوٓاْ إِلَّا لِيَعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ حُنَفَآءَ وَيُقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤۡتُواْ ٱلزَّكَوٰةَۚ وَذَٰلِكَ دِينُ ٱلۡقَيِّمَةِ ﴾ ۝٥

[سورة البينة]

((Kuma ba a umurce su da kome ba face su bauta wa Allah, su na ma su tsarkake addini gare shi ma su karkata zuwa ga addinin gaskiya, kuma su tsai da *Sallah* kuma su bayar da *Zakkah* kuma wannan shi ne addinin wadanda suke a kan hanyar kwarai))

Dalilin yin azumi fadar Allah Madaukaki:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُتِبَ عَلَيۡكُمُ ٱلصِّيَامُ كَمَا كُتِبَ عَلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَتَّقُونَ ١٨٣ ﴾ [سورة البقرة]

((Ya ku wadanda suka yi imani! An wajabta azumi a kanku kamar yadda aka wajabta shi a kan wadanda suke daga gabanninku, tsammaninku, za ku yi takawa.))

Dalili akan yin *Hajji* fadar Allah Madaukaki :

﴿ وَلِلَّهِ عَلَى ٱلنَّاسِ حِجُّ ٱلۡبَيۡتِ مَنِ ٱسۡتَطَاعَ إِلَيۡهِ سَبِيلٗاۚ وَمَن كَفَرَ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَنِيٌّ عَنِ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٩٧ ﴾ [سورة آل عمران]

((Allah ya wajabta yin *Hajji* a kan mutane, idan su na da halin, wanda ya bijirema umurnin Allah, to lalle Allah Mawadaci ne daga talikai"

Kashi Na Biyu: *Imani,* shi kuma ya kasu zuwa kashi saba'in da 'yan kai, mafi daukakarsu shi ne fadar " { لا إلــه إلا الله } (Babu abun bautawa da gaskiya sai Allah) kuma mafi karacinsa shi ne dauke kazanta daga hanya, kuma kunya wani sashe ne na imani."

Rukunnan Imani shida ne :

1 - Imani da Allah
2 - Imani da Mala'iku
3 - Imani da littattafai
4 - Imani da manzanni
5 - Imani da Ranar Lahira
6 - Imani da kaddara hairinsa da sharrinsa.

Dalili a kan wadannan rukunan shi ne fadar Allah Madaukaki:

﴿ لَّيۡسَ ٱلۡبِرَّ أَن تُوَلُّواْ وُجُوهَكُمۡ قِبَلَ ٱلۡمَشۡرِقِ وَٱلۡمَغۡرِبِ وَلَٰكِنَّ ٱلۡبِرَّ مَنۡ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ وَٱلۡكِتَٰبِ وَٱلنَّبِيِّـۧنَ ... ﴾ [سورة البقرة ١٧٧]

((Juyar da fuskokinku zuwa gabas da yamma ba shi ne addini ba, amma addini shi ne ga wanda yayi Imani da Allah da ranar lahira da mala iku da littattafan sama da annabawa.))

Dalili a kan yin imani da Kaddara shi ne fadar Allah Madaukaki:

﴿ إِنَّا كُلَّ شَيۡءٍ خَلَقۡنَٰهُ بِقَدَرٖ ﴿٤٩﴾ ﴾ [سورة القمر]

“ Lalle ne mu, kowane irin abu mun halitta shi a kan tsari”

Kashi Na Uku: *Ihsani,* wato kyautatawa .

Abinda a ke nufi da shi a nan, shi ne: ‘kabautawa Ubangiji kamar kana ganinSa, idan ya kasance ba ka ganinSa to lalle shi Ya na ganinka.

Dalili kuwa shi ne fadar Allah Madaukaki:

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلَّذِينَ ٱتَّقَواْ وَّٱلَّذِينَ هُم مُّحۡسِنُونَ ﴿١٢٨﴾ ﴾ [سورة النحل]

((Lalle ne Allah Ya na tare da wadanda suka yi takawa da wadanda su ke su masu kyautatawa ne))

da kuma fadar (Allah) Madaukaki:

﴿ وَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱلۡعَزِيزِ ٱلرَّحِيمِ ﴿٢١٧﴾ ٱلَّذِي يَرَىٰكَ حِينَ تَقُومُ ﴿٢١٨﴾ وَتَقَلُّبَكَ فِي ٱلسَّٰجِدِينَ ﴿٢١٩﴾ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ﴿٢٢٠﴾ ﴾ [سورة الشعراء]

((Ka dagara da Masbuwayi, Mai Jin kai, wanda Ya ke ganinka lokacin da kake tsaye da lokacin da kake

jjujjuyawa a cikin ma su sujada, lalle shi ya kasance Mai ji ne kuma Ma sani.))

Da Kuma fadar Ubangiji Madaukaki:

﴿ وَمَا تَكُونُ فِي شَأۡنٖ وَمَا تَتۡلُواْ مِنۡهُ مِن قُرۡءَانٖ وَلَا تَعۡمَلُونَ مِنۡ عَمَلٍ إِلَّا كُنَّا عَلَيۡكُمۡ شُهُودًا إِذۡ تُفِيضُونَ فِيهِۚ ... ﴾ [سورة يونس ٦١]

((Kuma ba ka kasance a cikin wani sha'ani ba, kuma ba ka karanta wani abin karatu ba, kuma ba kwa aikata wani aiki face Mun kasance tare da ku, lokacin da kuke tsunduma a cikinsa.))

Dalili a kan *Ihsani* (kyautatawa) daga *sunnah*, shine hadisin shahararren hadisin nan na Mala'ika Jibril, wanda umar dan Hattab (yardar Allah ta tabbata a gareshi) ya ce: "Mun kasance Muna zaune tare da Annabi (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi) sai wani mutum ya bullo mana sanye da tufafi fari fes, gashinsa baki wuluk, ba bu alamar tafiya a jikinsa, kuma ba bu wanda yasan shi a cikin mu, har sai da ya zauna kusa da Annabi , ya jingina gwuiwoyinsa da na Annabi ﷺ, ya dora hannayensa akan cinyoyinsa; sai yace: " ya *Muhammad* me ne ne Musulumci? Ya ce: "ka shaida babu wani abin bauta da gaskiya sai Allah, kuma hakika Annabi *Muhammad* manzon Allah ne, ka tsaida *Sallah*, ka bada *Zakkah* , kayi azumin Ramadhan, kuma ka yi *Hajji* idan kanada hali "

Sai yace: ‘Gaskiya ne.’
Sai muka yi mamaki yana tambayarsa kuma yana gaskata shi.
Sai yace masa : Me ne ne Imani ?
Ya ce: “Imani shi ne ka yi Imani da Allah, da mala ikunsa, da littattafansa, da Manzannisa , da Ranar Lahira, da Kaddara, ta alheri ko ta sharri.
Sai ya ce me ne ne kyautatawa (Ihsani)?
Ya ce: shine ka bautawa Allah kamar kana ganinsa in ba ka ganinSa, to shi yana ganinka.
Sai ya ce ma sa: yaushe ne lokacin alkiyama?
Ya ce: wanda a ke tambaya baifi wanda yake tambaya sanin lokacinta ba!

- Sai yace : bani labarin alamominta ?
- Yace za kaga baiwa ta haifi uwar gidanta, kuma za ka ga masu yawo ba takalmi, tsirara masu kiwon awaki, suna tsawaita gine-gine.
- Sai (Umar) ya ce: sai ya tafi; ni kuma na zauna tsawon lokaci.

SaiAnnabi yace: ya Umar ka san ko wa ne ne matanbayin?
Sai na ce: Allah da manzonsa suka sani.
Sai yace: wannan jibril kenan ya zo don ya sanar daku addininku”.

ASALI NA UKU :

Sanin Annabinku *Muhammad* ( tsira da Amincin Allah ya tabbata agareshi) shine : *Muhammad* dan Abdullahi dan Abdul Mutallib dan Hachim ( hachim daga kuraishi kuraish daga larabawa . larabawa daga zuria.

Ismail dan Ibrahim al halil , tsira da Amincin Allah yatabbata a gare su ) ya rayu shekara sittin da uku , arbain kafin annab- ta talatin da uku yana zaman Annabi kuma manzo.ya samu

Annabanci da { Igra } kuma ya samu manzontchi da ( Almudassir ) garinsa Makkah ; Allah ya domin yayi gargadi da barin shirki, yayi kira zuwa ga yin tauhidi . Dalili shi ne fadar Allah Madaukaki “

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡمُدَّثِّرُ ۝١ قُمۡ فَأَنذِرۡ ۝٢ وَرَبَّكَ فَكَبِّرۡ ۝٣ وَثِيَابَكَ فَطَهِّرۡ ۝٤ وَٱلرُّجۡزَ فَٱهۡجُرۡ ۝٥ وَلَا تَمۡنُن تَسۡتَكۡثِرُ ۝٦ وَلِرَبِّكَ فَٱصۡبِرۡ ۝٧ ﴾ [سورة المدثر]

“ Ma anar قم فأنذر tashi ka yi gargadi domin yin tauhidi tau da domin barin shirku وربك فكبر , ka permama Ubangiji da tauhidi وثيابك فطهر ka tsatkake tufafinka.

والرجر فاهجر kuma gumakai, sa ka kauzace musu , tare da ma abutansu – yayi shekara goma yana kira zuwa tauhidi , bayan haka an daga shi zuwa sama inda aka faralla mana salloli guda biyar. Ya

kasance yana *Sallah* a Makkah shekara uku, sai aka umurce shi da yin hijira zuwa Madina .

Mi nene hijira? Hijira shine barin garin da ake shirku zuwa garin da ake Musulumci.

Koma hijiri farilla ce akan al – uma. Kuma hukumcinta yananan hai alkiyama.

Dalili shine fadar Ubangiji Madaukaki Sarki :

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ تَوَفَّىٰهُمُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ ظَالِمِىٓ أَنفُسِهِمْ قَالُوا۟ فِيمَ كُنتُمْ ۖ قَالُوا۟ كُنَّا مُسْتَضْعَفِينَ فِى ٱلْأَرْضِ ۚ قَالُوٓا۟ أَلَمْ تَكُنْ أَرْضُ ٱللَّهِ وَٰسِعَةً فَتُهَاجِرُوا۟ فِيهَا ۚ فَأُو۟لَٰٓئِكَ مَأْوَىٰهُمْ جَهَنَّمُ ۖ وَسَآءَتْ مَصِيرًا ﴿٩٧﴾ إِلَّا ٱلْمُسْتَضْعَفِينَ مِنَ ٱلرِّجَالِ وَٱلنِّسَآءِ وَٱلْوِلْدَٰنِ لَا يَسْتَطِيعُونَ حِيلَةً وَلَا يَهْتَدُونَ سَبِيلًا ﴿٩٨﴾ فَأُو۟لَٰٓئِكَ عَسَى ٱللَّهُ أَن يَعْفُوَ عَنْهُمْ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَفُوًّا غَفُورًا ﴿٩٩﴾ ﴾ [سورة النساء]

((Lalle ne, wadanda mala'iku suka karbi rayukansu, alhali suna masu zaluntar kansu, su na ce musu : A cikin wane (yanayi) ku ka kasance? Su ka ce: mun kasance wadanda a ka raunana a cikin kasa. Su kuma su ka ce: ashe kasar Allah ba ta kasance mayalwaciyaba domin ku yi hijira a cikinta? To, wadannan makomarsu Jahannama ce. Kuma ta munana ta zama makoma. Face wadanda a ka raunana daga maza da mata da yara wadanda ba su iya yin wata dabara kuma ba su shiryuwa ga hanya.

To lalle wadannan akwai tsammanin Allah Ya yafe laifi daga gare su , kuma Allah ya kasance Mai yaifewa ne, Mai gafara ne.))

Da kuma fadar Allah Madaukaki:

﴿ يَٰعِبَادِيَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِنَّ أَرۡضِي وَٰسِعَةٞ فَإِيَّٰيَ فَٱعۡبُدُونِ ٥٦ ﴾[سورة العنكبوت]

((Ya bayi Na, wadanda suka yi imani! Lalle fa kasaTa mai yalwa ce, saboda haka ku bauta mi ni.))

AlBagawi (Allah Ya yi ma sa rahama) ya ce: Musabbabin saukar wanna ayar a kan musulmi ne wadanda suke Makkah ba su yi hijira ba, sai Allah ya kira su da sunan Imani.

Dalili akan umurni da yin hijira daga cikin sunna, shi ne fadar Annabi ﷺ "Hijira ba ta da karshe sai in tuba ya yanke, tuba kuwa bazai yanke ba sai rana ta hudo daga yamma."
Bayan Annabi yayi hijira zuwa madina an umurceshi da sauran hukumce hukumce, kamar *Zakkah*, da azumi kira zuwa ga haka, har Allah Ya yi masa cikawa kuma addininsa ya na nan kamar yanda ya zo dashi, kuma wannan shine addinin da ya zo da shi.
Babu wani alheri sai da bayyana shi, kuma babu wani sharri sai da yayi gargadi a kan sa.

Daga cikin abubuwan alheri akwai Tauhidi da kuma duk abubuwan da Allah ya ke so kuma yayarda da su.

Kuma daga cikin abubuwan sharri wadanda yayi gargadi da su akwai shirka da duk abubuwan da Allah ba ya so kuma Ya ke ki.
Allah ya aiko Annabinsa zuwa ga Mutane dukkansu, kuma yawajabta dukkan aljanu da mutune su yi ma sa biyayya.

Dalili shi ne fadar Allah Ubangiji Madaukaki:

﴿ قُلۡ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنِّي رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيۡكُمۡ جَمِيعًا ... ﴾

[سورة الأعراف ١٥٨]

((Ka ce ya ku matane lalle ni manzon Allah ne zuwa gare ku dukkanku.))

Kuma (Allah) Ya kammala addininSa da shi. Dalili kuwa shine fadar Allah Madaukaki:

﴿ ... ٱلۡيَوۡمَ أَكۡمَلۡتُ لَكُمۡ دِينَكُمۡ وَأَتۡمَمۡتُ عَلَيۡكُمۡ نِعۡمَتِي وَرَضِيتُ لَكُمُ ٱلۡإِسۡلَٰمَ دِينٗاۚ ... ﴾ [سورة المائدة ٣]

((A yau Na kammala ma ku addininku, kuma Na cika Ni'imata a kan ku, kuma Na yarda da Musulunci ya zama addini a gare ku.))

Da kuma Fadar Ubangiji Madaukaki:

﴿ إِنَّكَ مَيِّتٌ وَإِنَّهُم مَّيِّتُونَ ۝٣٠ ثُمَّ إِنَّكُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ عِندَ رَبِّكُمْ تَخْتَصِمُونَ ۝٣١ ﴾ [سورة الزمر]

((Lalle kai mai mutuwa ne, kuma su ma lalle masu mutuwa ne. Sa'an nan lalle ku a ranar kiyama a wurin Ubangijiku, za ku yi ta yin husuma.))

Kuma mutane idan su ka mutu za a tashe su, dalili shine fadar Allah Madaukaki:

﴿ مِنْهَا خَلَقْنَٰكُمْ وَفِيهَا نُعِيدُكُمْ وَمِنْهَا نُخْرِجُكُمْ تَارَةً أُخْرَىٰ ۝٥٥ ﴾ [سورة طه]

((Daga gare ta (kasa) Mu ka halitta ku , kuma a cikinta Mu ke mayar da ku, kuma daga gare ta Muke fitar da ku a wani lokaci na daban.))

Da kuma fadar Allah Madaukaki:

﴿ وَٱللَّهُ أَنۢبَتَكُم مِّنَ ٱلْأَرْضِ نَبَاتًا ۝١٧ ثُمَّ يُعِيدُكُمْ فِيهَا وَيُخْرِجُكُمْ إِخْرَاجًا ۝١٨ ﴾ [سورة نوح]

((Allah ne Ya tsiro da ku daga kasa tsirarwa. Sa'an nan ya mayar da ku cikinta, kuma ya fitar da ku fitarwa.))

Kuma bayan mutane sun taso ba yan mutuwarsu za a yi ma su hisabi, a ba wa kowa sakamakon aikinsa, dalili shine fadar Allah Madaukaki:

﴿ وَلِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِ لِيَجۡزِيَ ٱلَّذِينَ أَسَٰٓـُٔواْ بِمَا عَمِلُواْ وَيَجۡزِيَ ٱلَّذِينَ أَحۡسَنُواْ بِٱلۡحُسۡنَى ٣١ ﴾ [سورة النجم]

((Kuma abin da ke cikin sammai da abin da yake a cikin kasa na Allah kawai ne, domin Ya sakawa wadanda suka munana da abin da suka aikata, kuma Ya sakawa wadanda suka kyautata da sakamakon da ya fi kyau.))

Wanda ya karyata da cewa za a tashi bayan mutuwa, ya kafirta. Dalili shi ne fadar Allah Madaukaki:

﴿ زَعَمَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَن لَّن يُبۡعَثُواْۚ قُلۡ بَلَىٰ وَرَبِّي لَتُبۡعَثُنَّ ثُمَّ لَتُنَبَّؤُنَّ بِمَا عَمِلۡتُمۡۚ وَذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٞ ٧ ﴾ [سورة التغابن]

((Wadanda suka kafirta sun ce ba za a tayar da su ba. Ka ce: ‘Na rantse da Ubangijina, lalle za a tayar da ku, sa’annan kuma lalle a ba ku labari game da abin da ku ka aikata. Kuma wannan ga Allah mai sauki ne.”

Allah ne ya aiko da Manzanni dukkanin su, domin suyi albishiri kuma su yi gargadi; Dalili shi ne fadar Allah Madaukaki:

﴿ رُّسُلٗا مُّبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ لِئَلَّا يَكُونَ لِلنَّاسِ عَلَى ٱللَّهِ حُجَّةُۢ بَعۡدَ ٱلرُّسُلِۚ ... ﴾ [سورة النساء ١٦٥]

((Manzanni masu bushara kuma ma su gargadi, domin kada wata hujja ta kasance ga mutane a kan Allah bayan (aiko) manzannin.))

Na farkonsu shi ne Annabi nuhu. Allah Madaukaki Ya ce:

﴿ إِنَّآ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ كَمَآ أَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰ نُوحٖ وَٱلنَّبِيِّـۧنَ مِنۢ بَعۡدِهِۦۚ ... ﴾ [سورة النساء ١٦٣]

((Lalle ne Mu, Mun yi wahayi zuwa gare ka, kamar yadda muka yi wahayi ga Nuhu da Annabawa daga bayansa.”

Kuma ko wacce al’umma Allah ya aiko ma ta manzo, tun daga al’ummar Annabi nuhu, har zuwa ga al’ummar Annabi *Muhammad* ﷺ, su na umurninsu da yin ibada ga Allah shi daya, kuma su na hana su bautar gumaka, dalili shi ne fadar Allah Madaukaki:

﴿ وَلَقَدۡ بَعَثۡنَا فِي كُلِّ أُمَّةٖ رَّسُولًا أَنِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱجۡتَنِبُواْ ٱلطَّٰغُوتَۖ... ﴾ [سورة النحل ٣٦]

((Kuma lalle ne, mun aika da wani manzo a cikin kowace al umma ( ya na cewa:) ‘ku bauta wa Allah, kuma ku nisanui Tagutu’))

Kuma Allah ya wajabtawa dukka bayi cewa su kafirta da Tagutu kuma su yi imani da Allah shi kadai.

Ibn kayyim (Allah ya ramahamce shi ) yace : “Tagutu shi ne: ‘duk abin da bawa ya girmama shi har ketare iyakarsa, sawa’un ya zamanto abin bauta ne ko kuwa abin yi ma biyayya ne .
Kuma Taguta ya na da yawa, amma mafi munin su, biyar ne:

1 - Iblis (Allah yala’ance shi )
2 - Wanda ya yarda ake bauta masa
3 - Wanda ya kira mutane domin su bauta masa
4 - Sai wanda yace shi ya san gaibu
5 - Sai wanda yayi hukumci ba da abin da Allah ya saukar ba dalili kuwa shi ne fadar Allah Madaukaki:

﴿ لَآ إِكۡرَاهَ فِي ٱلدِّينِۖ قَد تَّبَيَّنَ ٱلرُّشۡدُ مِنَ ٱلۡغَيِّۚ فَمَن يَكۡفُرۡ بِٱلطَّٰغُوتِ وَيُؤۡمِنۢ بِٱللَّهِ فَقَدِ ٱسۡتَمۡسَكَ بِٱلۡعُرۡوَةِ ٱلۡوُثۡقَىٰ لَا ٱنفِصَامَ لَهَاۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ٢٥٦ ﴾ [سورة البقرة]

((Babu tilastawa a cikin addini, hakika, shiriya ta bayyana daga bata: saboda haka wanda ya kafirta da tagutu kuma ya yi imani da Allah, to hakika yayi riko ga igiya ammintacciya, babu yankewa a gare ta. Kuma Allah mai ji ne masani ne.))

Wannan shine ma’anar لا إله إلا الله “ babu abin bauta da gaskiya sai Allah” kuma hadisi ya ce: “Musulumci shi ne kan alamurin. Kuma *Sallah* ce ginshikin sa, jihadi *fi sablililahi* kololuwarsu”

Allah shine masani .

Wannan shi ne Karshen Littafin.